JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA ٢١ Ramadhan, 1443

MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI ٢٢ Afrilu. 2022

## KWANAKI GOMAN ƘARSHE DA FIƘIHUN MUHIMMAN ABUBUWA A RAYUWAR ZAMANINMU

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ku yi gaggawa wajen yin rige-rige zuwa ga wata gafara daga Ubangijinku, da kuma aljannar da take da faɗi matuƙa, faɗin nata kamar sammai da ƙasa, an samar da ita ne saboda waɗanda suka gasgata Allah da Manzannisa, lallai wannan babban sakamako falala ne daga Allah, da yake bayar da ita ga wanda ya so a cikin bayinsa, lallai Allah shi kaɗai ne mai falalar da ta fi ƙarfin tunani ya sifanta)** [al- Hadid: 21], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai a cikin rahamar da Allah Maɗaukakin Sarki yake yi wa bayinsa ne ya samar masu da ranaku goma na ƙarshen watan Ramadhan masu albarka, ranaku ne da Allah yake ruɓanya ladan kyawawan ayyuka, ranaku ne da ake rige- rige zuwa ga gabatar da ayyukan alhairi, lokaci ne da rayuka suke ƙara samun nishaɗi ganin cewa an zo daf da ƙarshen watan, lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana matuƙar kyautata amfana da waɗannan kwanaki masu falala, an ruwaito Sayyida

A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana ƙara ijtihadi a kwanaki goman ƙarshen da bay a yin irinsa a wasu kwanakin)** haka ma tana cewa**: (Idan an shiga goman ƙarshe Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan raya dare, ya kuma tashi iyalansa, ya kuma zage dantse ya yi ta ƙoƙari).**

A cikin kyautata koyi da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), akwai raya darare goma na ƙarshen Ramadhan ta hanyar yawaita sallah, da karatun Alƙur'ani, da zikiri, da neman gafara, da ciyarwa a hanyoyin alhairai, waɗannan ɗabi'u ne na salihan bayin Allah, bauta ce ta masu tsoron Allah, Allah mai girma da ɗaukaka ya sifanta 'yan aljanna da cewa: **(Haƙarƙarinsu suna nisantar wuraren kwanciya, suna roƙon Ubangijinsu cikin tsoro da kyautata fata, kuma suna ciryawa daga cikin abin da muka azurta su. Saboda haka wani rai bai san abin da aka ɓoye musu na kwanciyar hankali, sakamako abin da suka kasance suna aikatawa)** [as- Sajada: 16 -17], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya sifanta masu tsoron Allah da cewa: **(Lallai waɗanda suka bi Allah, suka kuma ji tsoronsa za su ji daɗinsu a cikin aljanna da idanuwan ruwa da ba a iya misalta su. Suna amsar abubuwan da Ubangijinsu ya ba su na lada da karramawa, lallai su a duniya suna kyautata bayar da abubuwan da aka nema daga gare su kafin wannan lokaci. Sun kasance suna barci kaɗan ne da daddare, a mafi yawan daren kuma suna tashi domin gabatar da ibada. A ƙarshe-ƙarshen daren kuma suna neman gafara)** [az Zariyat: 15 -18], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Na hore ku da yin ƙiyamullaili, saboda tada ne na salihan bayin Allah da suka gabace ku, hanya ne na ƙara samun kusanci da Allah, da kuma**

**kawo ƙarshen aikata zunubi, suna kuma kankare munanan ayyuka, suka kuma tsarkake jiki daga dukan cuta).**

Ganin cewa watan Ramadhan wata ne na samun ʻyanci ga barin wuta, kuma babu wani dare a cikin dararensa da zai zo face Allah mai girma da buwaya ya ʻyanta bayi da yawa daga shiga wuta, to kuwa an fi tsammanin haka da fatansa a cikin waɗannan kwanaki goman, tun da Allah Ubangijinmu yana gafarta wa masu neman gafararsa a lokutan sahur, to kuwa an fi tsammani da fatan samun gafara da rahama a cikin waɗannan kwanaki goman, saboda ƙunshe suke da wani dare da Allah mai girma da buwaya ya karrama shi, ya kuma fifita shi akan sauran darare, wannan daren kuwa shi ne daren Lailatul Ƙadri, inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Ku nemi Lailatul Ƙadri a cikin kwanaki goman ƙarshe na Ramadhan).**

Wannan daren shi ne Sarki a cikin darare, wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da littafinsa mai girma da daraja, ta hanyar mala'ika mai girma da daraja, zuwa ga al'umma mai girma da daraja, dare ne da gafara da rahama da albarka suke sauka, Allah mai gima da ɗaukaka yana cewa: **(Mu kam mun saukar da Alƙur'ãni ne a wani dare mai daraja da girma. Kai dai ba ka san dare mai daraja da girma ba ne!.. Ai wannan daren mai daraja da girma, matsayinsa da darajarsa ya zarce watanni dubu, saboda Allah ya keɓance shi da saukar da Alƙur'ãni Mai girma!.. Mala'iku har da Jibrilu (Alaihimus-Salam) suna sauka ƙasa a cikinsa da izinin Allah, saboda dukanin wani umurni.. Wannan dare aminci ne ga barin duk wani abu mai cutarwa, har zuwa lokacin fitowar alfijiri)** [al- Ƙadri: 1- 5], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya**

**raya dare Lailatul Ƙadri yana cike da imani da kuma neman lada a wurin Allah, za a gafarta masa zunubansa da suka gabata).**

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa hadīn kai da gyara tsakanin masu husuma da juna hanyoyi ne na samun karɓuwar ayyuka na gari, su kuwa saɓani da rikici hanyoyi ne na rashin samun karɓuwar ayyuka, musamman a waɗannan darare masu falala, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Na fito ne saboda in faɗa maku wane dare ne daren Lailatul Ƙadri, sai na tarar da wane da wane suna faɗa da juna, sai aka ɗauke daren, ta yiwu ɗauke daren ya zama alhairi a gare ku),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(A cikin watan akwai daren da alhairansa suka fi na watanni dubu, duk wanda aka haramta masa alhairan ciki, to kuwa lallai an haramta masa alhairi).**

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Ganin cewa ƙofofin ayyukan biyayya da ɗa'a a waɗannan kwananki masu albarka suna da yawa, to lallai mai hankali shi ne zai tsara abubuwan da suka fi dacewa da shi a cikinsu, ya gabatar da abubuwan da suka kama a gabatar, waɗanda amfaninsu yake da faɗi akan abubuwan da amfaninsu ya ƙuntata; saboda haka fitar da zakkar kono ta fi tabbata a cikin waɗannan kwanaki, ya kuma kamata a gaggauta fitar da ita gab da sallar Idi, saboda ya yalwata wa talakawa da miskinai, da marayu da mabuƙata, inda hakan zai ba mu daman biya masu buƙatunsu tun kafin idi ya

shigo, Annabimu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa**: (Ku wadatar da su ga barin roƙo ko nema a wannan rana),** ya kuma halatta a fitar da zakkar kono da kuɗi, gwargwadon ƙimar zakkar, hasali ma kuɗin ya fi amfanar talakawa a wannan zamani da muke ciki, ya fi biya masu buƙatunsu, saboda lura da irin yanda hakan ya fi amfanar talakawa, idan muka yi la'akari da manufofin Shari'a.

Haka ma Fiƙihun jere abubuwa daidai da amfaninsu zai wajabta gabatar da ciyar da talakawa da miskinai da yalwata wa mabuƙata akan yawan maimaita ayyukan Hajji da Umura, na farkon wajibi da yake akan kowa, ko wanda waɗansu suke ɗauke wa wasu, na biyun kuma nafila ne, kuma babu shakka ana gabatar da wajibin da yake akan kowa, ko wanda yake akan ɗaukacin al'umma akan sauran nafilfili, bugu da ƙari ga kuma lada mai girma da yake tattare da yaye damuwa da baƙin cikin waɗanda suke cikin damuwa da baƙin ciki, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da Allah ya fi sonsa a cikin mutane shi ne wanda ya fi amfanar mutane, kuma aikin da Allah ya fi so a cikin ayyuka shi ne farin cikin da za ka shigar a cikin zuciyar Musulmi, ko ka yaye masa damuwa, ko ka biya masa bashin da ake binsa, ko ka kori yunwar da take damunsa),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa**: (Duk wanda yay aye wa mumini wata damuwa daga cikin damuwar duniya, to kuwa Allah zai yaye masa damuwa daga cikin damuwar ranar alƙiyama).**

**Ya Allah Ubangijinmu ka amshi azuminmu da ƙiyamullalin da muke yi, ka kuma kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**